taimakon su". Bakara: 48

**Ranar Sakamako** Ranar sakamako; Ita ce ranar da za a tara aljanu da mutane domin saka musu da abin da suka aikata a wannan duniya na biyayya ko sabawa. Akwai dalilai masu yawa na hankali da na shari'a game da rananr sakamako, amma kasancewar kura'ani mai girma da ruwayoyin da suka zo daga Annabi (S.A.W) game da ranar alkiyama suna da yawan gaske, sannan imani da wannan rana bisa dogaro da su wani abu ne sananne gun musulmi gaba daya, don haka zamu yi nuni da wasu daga dalilan hankali game da haka:

**Dalilin Adalci** Kasancewar ubangiji wajibi ne ya siffantu da adalci, ya wajabta zuwan ranar alkiyama domin tsayar da adalci tsakanin mai zalunci da wanda aka zalunta. Idan adalci shi ne ba wa duk mai hakki hakkinsa, to wannan yana tilasta karbar hakki daga hannun azzalumi da mayar da shi hannun ma'abocinsa na ainihi. Don haka ne koton Allah mai hukunci da adalci zata zauna a wannan rana domin tsayar da adalci da sakamako da abin da bayi suka aikata na alheri da na sharri.
Haka nan kasancewar ubangiji mai hikima da adalci ya lizimta rashin daidaita tsakanin azzalumi da wanda aka zalunta a sakamakon, don haka dole ne a samu wata rana da za a karbi hakkin mai hakki a mayar da shi ga mai shi na asali.
Da yake zalunci bai takaita da abin da yake faruwa tsakanin bayi ba na danniya da fın karfı, don haka zalunci yana iya kasancewa cikin abin da ya shafi daidaita mai kyautatawa da mai munanawa, don haka tunda daidaita mai aikata alheri da mai aikata sharri a sakamako yana daga zalunci, don haka ya zama wajibi ga Allah ya zo da wata rana da zai ba wa kowanne daga cikinsu abin da ya cancance shi, domin rashin samar da wannan rana domin sakamako da abin da ya cancanta ga wadannan bangarori biyu, ya zama daidaita su a sakamako wanda ya gabata cewa yin hakan zalunci ne, shi kuwa ubangiji ya kubuta daga yin zalunci.

**Dalilin Koruwar Wasa** Mahangarmu game da ayyukan ubangiji madaukaki ita ce; cewa shi ba mai wasa ba ne, kuma wasa ya koru daga ayyukansa, saboda haka halittar duniya musamman halittun da suke da zabi a ayyukansu kamar 'yan Adam da aljanu duk ba domin wasa ba ne, don haka dole ne a samu wata rana da zasu taru wuri daya domin sakamakon abin da suka aiwatar da wanda suka aikta a wannan rayuwa ta duniya. Da halittar mutum da aljan ta takaita da duniya ne kawai da wannan ya lizimta wasa a ayyukan Allah (S.W.T) alhlin wasa ya koru gareshi madaukaki.

**Dalilin Hadafi** Akwai wasu jama'a daga Ash'ariyya da suka tafi a kan cewa; ayyukan Allah (S.W.T) ba su da hadafi, don haka mun saba da su a kan haka. Mahangarmu ita ce; ayyukan Allah suna da hadafi.

A bisa wannan dalilin ne muke cewa: tun da wasa ya koru ga Allah (S.W.T) kamar yadda ya gabata a dalili na sama, saboda haka wannan halitta da Allah ya yi tana da hadafi, kuma tunda mun ga wannan hadafin, na kamala ne ko na sakamako ba zai iya samuwa a wannan duniyar ba, don haka dole ne a samu wata duniyar daban da take da yanayin da ta cancanci tabbatar wannan hadafin a cikinta.

**Hadafin Sakamakon Ayyuka** Ubangiji madaukaki ya halicci mutum da aljan domin hadafi da yake son su kai zuwa gareshi na kamala, wannan ya sanya kallafawa bayi ayyuka da nauyi mai girma kamar wajabin salla, da zakka, da azumi, da hajji, da umarni da kyakkyawa da hani da mummuna. Da kuma ayyukan da ya haramta kamar shan giya, da zina, da cin kudin riba, wannan duk domin su sami kaiwa zuwa ga wannan matsayi mai girma na kamala.

Amma bayi ba su zamanto daya ba a cikin karbar wannan sakon, acikinsu akwai; mai sabo da mai biyayya, don haka ya zama wajibi a samu wata rana da za a saka wa kowanne daga cikinsu da abin da ya cancanta da shi na kamala ko kaskanci sakamakon ayyukansu da karbarsu ga wannan takalifi da aka dora musu ko rashin karbarsu gareshi.

**Hadafin Kamala Da Sa'ada** Tunda ubangiji ya halicci mutum da aljan domin su samu kamala da sa'ada ne da suka cancance su, wannan kuwa ba mai samuwa ba ne a wannan duniya kamar yadda muke iya ganin halin duniya na canje-canje, da karewa, da wahala, da tsufa, da rauni, don haka ne dole a samu wata duniya daban ba wannan ba, da take da yanayin da ya .dace da kamala da sa'adar da ta cancance su